

Ire-iren Noma

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin  koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: •    San amon sautukan haruffan Hausa; •    Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Ire-iren Noma
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor


Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants

Nas Yakubu Bloom Trainer

Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi

Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright: SIL International 2009








Noma iri biyu ne.
Akwai noman tsirrai.
Haka akwai kiwon dabbobi.
Kowanne yana da amfani.
Kowanne ya dogara kan ɗaya.


Noman tsirrai shi ne na shuka iri.
Akan shuka irin gero.
Akan shuka irin dawa.
Akan shuka irin masara.
Akan ma shuka shinkafa da alkama.
Ana yi domin mutum ya amfana.



















Kiwo shi ne renon dabbobi.
Akan yi kiwon shanu da awaki.
Akan yi kiwon raguna da tumaki.
Akan yi kiwon kaji da kifi.
Ana yi domin mutum ya amfana.

Noman tsirrai akan yi shi lokacin damina.
Akan yin shi ma lokacin rani.
Kiwon  dabbobi akan yi shi kowane lokaci.
Damina shi ne lokacin ruwan sama.
Rani shi ne lokacin da ba ruwan sama.












Kowane irin noma ya na da amfani.
Da noma mu ke samun abinci.
Da noma mu ke samun sutura.
Noma ke ba mu magani.
Noma ke ba mu gidaje.
Komai ma sai da noma.


Kowa ya dogara ga noma.
Malamin makaranta ya dogara ga noma.
Likita ya dogara ga noma.
Injiniya ya dogara ga noma.
Ɗan kasuwa ya dogara ga noma.
Masunci ya dogara ga noma.
Idan babu noma babu rayuwa.




ni ka sa ra
i kan si ri
ni i ni







ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT
USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE
World Vision
Australian Aid
GLOBAL READING NETWORK